*Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 008 (Pg. 86-92)*

# Kyautata Ɗabi'u Da Hanyoyin Inganta su ga Ɗalibai: Ɗauki daga Taskar Rubutattun Waƙoƙi

**Muhammad Awal Inuwa**
awalinuwa@gmail.com
*08036368426*
Department of Arts Education
Hausa Section
Federal University of Education, Kontagora

## Abstract

*Self-discipline, tolerance are parts of the ingredients for attaining positive character development among the students of higher Nigeria. Nowadays character development, have become imperative for a successful and satisfactory graduate. Today the issue of positive character development is at a worrisome stage in various institution of higher learning. Many students have been caught in cultism, exam malpractice, drug abuses, armed robbery and other related social vices. This gives bad image to their institution and the country at large. This paper therefore examines the prospect of Hausa written poetry to enhance positive character among the students especially when the message derived from the poems are put in use. Poems from the artistic works of Hausa poets will be cited in this paper.*

**Key words:** *Ɗabi'u, Ɗalibai, Rubutattun Waƙoƙi.*

## *Tsakure*

*Kyakkyawan ɗabi'a kamar haƙuri suna daga cikin hanyoyin samar da ingattacciyar tarbiyya ga ɗaliban manyan makarantu a Nijeriya. Kyakkawan ɗabi'a da tarbiyya ta gari suna daga cikin sharuɗan samun takardar shaidar kammala karatu. A wannan zamani taɓarɓarewar tarbiyya da kyawawan ɗabi'u abu ne da yake matuƙar damuwa a manyan makarantunmu. Domin an sha kama ɗalibai da hannu dumu-dumu a cikin ƙungiyoyin asiri da satar jarabawa da tu'ammali da miyagun ƙwayoyi da fashi da makami da sauran miyagun ɗabi'u. Waɗannan miyagun ɗabi'u suna ɓata sunan makaranta da ma ƙasa baki ɗaya. Don haka ne wannan muƙala ta yi amfani da rubutattun waƙoƙi a matsayin hanyar kyautata ɗabi'un ɗalibai da ingantan su, musamman idan aka yi amfani da darussan da suke koyarwa.*

**Fitillun kalmomi:** *Ɗabi'u, Ɗalibai, Rubutattun Waƙo*ƙi

## Gabatarwa

Satar jarabawa da shaye-shaye da sace-sace da shiga ƙungiyoyin asiri da sauran makamantansu suna ƙara yawaita a Jami'o'i da Kwalejojin ilmi da makarantun Kimiyya da Fasaha da sauran ire-irensu a wannan ƙasa (NIjeriya). An sha samun ɗalibai da hannu dumu-dumu a cikin waɗannan miyagun ayyukan wanda hakan ba ƙaramar illa ba ce ga harkar ilmi da ci gaban ƙasa.

Kasancewar kyawawan ɗabi'u da halaye na gari suna daga cikin sharuɗan da ɗalibai ya kamata su cika kafin kammala karatunsu, ya sa wannan muƙalar take da ra'ayin cewa,

"Rubutattun Waƙoƙin Hausa" suna da rawar da za su iya takawa wajen jawo hankalin ɗalibai tare da cusa kyawawan ɗabi'un da ake so su kasance suna da su muddin dai za a yi aiki da saƙo da suke ɗauke da shi. A yayin gudanar da wannan aiki za a yi taƙaitaccen bayani a kan waƙa da muhimmancinta, sannan kuma za a kawo wasu baitoci da suke nuni a kan yadda ya kamata ɗalibi na gari ya kasance tare da yin taƙaitaccen sharhi daga ƙarshe sai kuma kammalawa da shawarwari.

## Manufar Wannan Bincike

Manufar aiwatar da wannan bincike ita ce, fito da yadda rubutattun waƙoƙi na Hausa suke ba da gudummuwa wajen inganta tarbiyya a manyan makarantu. Sannan tare da duba saƙonnin waƙoƙin za su yi tasiri wajen cusa ɗa'a da kyawawan ɗabi'u da halaye na gari a tsakanin ɗalibai a manyan makarantu. Haka kuma binciken zai fito da miyagun ɗabi'u da suke gudanar a wannan makarantu da nufin hannunka mai sanda domin ƙaurace masu. Fito da yadda za a sa ɗalibai su riƙa bin dokokin makaranta sau da kafa tare kauce wa miyagun ayyuka domin ci gaban al'umma.

## Dabarun Gudanar da Bincike

A fannin aiwatar da bincike akwai hanyoyi da yawa da ake bi wajen tattaro bayanai, waɗanda za su taimaka wa mai bincike ya cimma burinsa. A wannan bincike an yi amfani da dabarar nazarin rubutattun waƙoƙin Hausa waɗanda suke ɗauke da saƙon da muƙalar take son isarwa. Bayan wannan kuma an yi amfani da kafar sadarwa ta intanet wajen farautar bayanai masu alaƙa da wannan bincike. Kasancewar ita ce hanya ta zamani, kuma Hausawa sun ce, zamani abokin tafiya.

## Farfajiyar Bincike

Kasancewar tarbiyya aikin kowa ne a cikin al'umma, wanda ya haɗa har da malaman makaranta da maƙwabata da `yan`uwa da sauran jama'a. Haka kuma lalacewar tarbiyya da miyagun ɗabi'u suna shafar kowa a cikin al'umma. Sannan miyagun ɗabi'u a tsakanin ɗalibai sun zama ruwan dare, da wannan ne aka iyakance wannan bincike akan ɗaliban manyan makarantun na gaba da sakandare. Binciken ya zaɓi waɗannan rukuni ne na makarantu saboda a nan aka fi bayyana irin waɗannan miyagun halaye na rashin ɗa'a a fili.

## Ra'in Bincike

An ɗora wannan bincike a kan ra'in tanƙwasa ɗan'adam (Social Control Theory). Wannan ra'i yana bayanin yadda ake amfani da wasu abubuwa domin tanƙwasa mutum ya yi biyayya ga abin da al'umma ke so, wato waɗanda ake gani a matsayin halayen kirki (Ado, 2019:128). Da wannan ne masana irin su Otitie da Ogionwo (1981:375) sun bayyana cewa, duk al'ummar da take son zaman lafiya da kwanciyar hankali dole ta kasance tana shimfiɗaɗɗun dokoki da aka yarda a bi su domin su zama hanyar tanƙwarawa da daidaita ɗabi'un mutane. Shi dai wannan ra'i wani masani ɗan ƙasar Amurka ya ƙirƙire shi mai suna Edward Ross a shekarar (1910). Sannan kuma shi ya fara amfani da shi wajen nazarin zamantakewar al'umma da halayyar mutanen da ke cikinta (Sociology). Don haka aka ga ya dace a yi amfani da wannan ra'i domin nazarin yadda

za a inganta kyawawan ɗabi'u a manyan makarantu. Wannan ra'i ya yi daidai da karin maganar Hausawa da ke cewa, "ice tun" yana ɗanye ake tanƙwasa shi. Haka nan wannan ra'i zai taimaka wajen nuna yadda kyawawan ɗabi'u da ɗalibai za su koya a saƙon rubutattun waƙoƙin Hausa zai samar da zaman lafiya a cikin al'umma. Da wannan ra'i ne za a yanken hukuncin wannan bincike.

## Ma'anar Waƙa

Waƙa wasu zantuttuka ne da mawaƙi ke amfani da su don isar da saƙo da ke ƙunshe da rauji, saɓanin maganar yau da kullum. Wannan saƙon na iya kasancewa faɗakarwa ko ilmantarwa ko tunatarwa ko gargaɗi ko nishaɗantarwa ko wani makamancin haka. Yahaya (1997) a riwayar Inuwa (2008) ya bayyana waƙa a matsayin wata tsararriyar maganar hikima da ta ƙunshi saƙo cikin zaɓaɓɓun kalmomi da aka auna domin maganar ta reru ba faɗa kurum ba. Shi ko Ɗangambo (2007) yana cewa, waƙa wasi saƙo ne da ake gina shi kan tsararriyar ƙa'ida da baiti, da ɗango da reraawa da kari (Bahari) amsa-amo (ƙafiya da sauran ƙa'idoji da suka shafi daidaita kalmomi da zaɓansu da amfani da su cikin sigogin da ba lalle haka suke a maganar baka ba. Masana sun raba waƙa zuwa giuda biyu, waƙar baka da rubutacciyar waƙa. Wannan muƙala za ta dubi rubutacciyar waƙa ce.

## Rubutacciyar Waƙa

Rubutacciyar waƙa ita ce waƙar da aka shirya aka tsara a rubuce domin karantawa. Muktar (2005) yana cewa rubutacciyyar waƙa wata hanya ce ta gabatar da wani saƙo a cikin ƙayyadaddun kalmomin da aka zaɓa waɗanda ake rerawa a kan kari da ƙafiya a cikin baitoci. Sho ko Bunza (1996) a riwayar Inuwa (2012) cewa ya yi rubutacciyar waƙa zancen hikima ce da aka ɗora cikin rubutaccen tsari tare da la'akari da Zubin kalmomin da tsarinsu da ƙafiyarsu da kuma yawan layukansu ko sheɗaransu. A cewarsa duk waƙar da aka tsara bisa wannan tsari ita ake kira da suna rubutacciyar waƙa. Masana adabi da tarihin rubuce-rubucen Hausa sun nuna cewa rubutacciyar waƙa ta fara samuwa tun cikin ƙarni na 17 bayan da addinin Musulunci ya fara zama a ƙasar Hausa.

An fara samun yawaitar rubutattun waƙoƙin Hausa ne da bazuwarsu a ƙarni na 19 bayan jihadin Mujaddadi Shehu Usmanu Ɗanfodiyo da almajiransa. A ƙarni na ashirin ne rawa ta kaure a tarihin rubutattun waƙoƙin Hausa domin a lokacin ne aka samu gagarumin yawaitar rubutattun waƙoƙin Hausa ko'ina. Wannan ko ba ya rasa nasaba da shigowar Turawa a ƙasar Hausa, waɗanda suka shigo da abubuwa daban-daban. Haka dai abin ya yi ta tafiya har zuwa yanzu buatoci suna tasowa ana samun mawaƙa suna bake kolin tunanensu wajen waƙesu. Jigogin waƙoƙin ƙarni na goma sha tara an samu ƙaruwar wasu jigogi wajen rubuta su, kamar ilmantarwa a kan ilmin zamani da zamantakewa da ƙere-ƙere da kishin ƙasa da kishin harshe da siyasa ta aƙida da ta jam'iyya da soyayya da sauransu.

Rubutacciyar waƙa kamar sauran ɓangarorin adabi tana da matuƙar muhimmanci fagen raya al'adu da inganta su da kyautata zamantakewar al'umma da wa'azantarwa ko faɗakarwa a kan horo da aikata alheri ko

hani da aikata munanan abubuwa. Hakazalika, takan kasance taskar adana tarihi da koyar da harrshe. Har ila yau, takan kasance tubalin samar da zaman lafiya da bunƙasar tattalin arziki. Haka takan kasance igiyyar ƙulla zumunta da sadar da ita. Wani muhimmin aiki rubutacciyar waƙa shi ne wayar da kan jama'a da yaɗa manufofin gwamnati da na siyasa da sauran makamantan haka.

**Rubutacciyar Waƙa A fagen Kyawawan Ɗabi'u ga Ɗalibai**

Kasancewar waƙa aba ce nai matuƙar tasiri ga rayuwar al'umma yasa marubuta waƙoƙin Hausa suke rubuta waƙoƙi don jawo hankalin ɗalibai da sauran yara ko matasa a kan su zamo mutanen kirki masu kyawawan ɗabi'u da halaye na gari, tare da watsi da duk wata ɗabi'a mummuna da ka iya kai su ya baro. Mawaƙa da dama sun yi irin waɗannan rubuce-rubuce. Salihu Kwantagora yana ɗaya daga cikin waɗannan mawaƙa. Ga dai abin da yake cewa:

"Ina `yan`uwa na ku zo ku jiya,
Ɗabi'a ta yaron ƙwarai nagari.
A yau shi ne nike so in ba ku bayani,
Nike so ku koya ku zan nagari.
Abin sha'awa ne abin marmari,
Ga yaro da yazzam mutum nagari.
A kan zam ana sha'awa tasa kulum,
Idan ya kasance nagari."

Idan aka dubi waɗannan baitocin za a ga cewa, mawaƙin yana jawo hankali tare da yin kira a kan muhimmancin zama nagari; duk da cewa mawaƙin ya yi amfaani da kalmar yaro a cikin baitocin to haƙiƙanin gaskiya abin ba a kan yara kawai ya tsaya ba.

**Ɗabi'u da Halaye na Ƙwarai**

A nan mawaƙin ya kawo wasu ɗabi'u da halayen yaron ƙwarai da ya kamata duk dalibi nagari ya kasance ya yi koyi da su kamar kiyaye abubuwa marasa kyau da rashin yin faɗa da fushi da zuwa aji cikin natsuwa da tsafta haka ba ya raina `yan uwansa ɗalibai da malamansa da sauran shugabanni. Haƙiƙa waɗannan abubuwan ne da za su taimaka wajen inganta tarbiyya. Ga abin da ya ce:

"Abin duk da ba shi da kyau ya sani,
Yakan guji son aukuwan tunzura.
Idan ya yi laifi shi kan yi nadama,
Shi kan ba da hujjan shi ko hanzari.
Yakan zama ba mai fushi ko faɗa,
Irin na kare, ba shi son tunzari.
Yakan ƙi abokai da ba su kula,
Da haƙƙin mutuncin mutumin gari.
Ayyukansa kullum abin so ga kowa,
Mutane suna son shi duk a gari.
Shi kan zo aji a cikin natsuwa,
Da tsafta da duuk haluka na gari.
Ba zai raina dangi bale malamai,
Da minita da hediboyi duk nagari".

**Miyagun Ɗabi'u**

Mawaƙin ya kawo wasu baituka da ke ƙunshe da wasu miyagun ɗabi'u da halaye da wasu yaran banza masara kirki ke aikatawa kamar haka:

"Ina so in ganar da almajirai,
Waɗansu abin ƙinmu ɓata gari.
Waɗannan da ba su da kishi a zuci,
Marasa kasalar shiga hatsari.
Da ka gan su ba su da niyyar ƙwarai,
Fa sai nuna tsiwa ga manyan gari.
Fa su ne fitilllu wurin zanga-zanga,
Da zafin husuma ga mayan gari.

Idan ka ji an ce ana zanga-zanga,
Fa su ka shirya a yo tunzura.
Su kan ɓata kayan gwamnati ta yi,
Da tai tangiya don ta gyara gari.
Su ka zagin manya su raina hukuma,
Su raina iyayensu ɓata gari".
Haka ya ci gaba da cewa:
Fa su ne ɓarayi kaza `yan fashi
Fa sun shiga yawo gari ya gari
Ga mata irin su fane karuwai
Giya ce abincinsu ɓata gari.
Abincinsu taba wui-wui da ƙwaya
Su sha sui ta maye suna garari."

Waɗannan baitoci sun fito da miyagun ɗabi'u waɗanda suke tunzura masu aikata ɓarna a cikin makaranta ko a gari kamar rashin girmama na gaba da shirya zanga-zanga da shaye-shayen ƙwayoyi da wui-wui da giya tare da ɓata kayan gwamnati da aka samar don kyautata rayuwar al'umma da sauaransu. Mawaƙin ya nuna wani lokaci su ne ake samu da aikata sace-sace da fashi da makami. Idan aka kalli waɗannan abubuwa da idanun basira za a ga cewa duk suna aukuwa a manyan makarantu na gaba da sakadire kai har ma da sakandire. Mawaƙin bai tsaya nan ba, sai da ya kawo wasu baitoci da masu kira tare da jan hankali wajen nisantar tare da ƙaurace wa waɗannan miyagun abubuwa ga dai abin da yake cewa:

"Ku nisanci duk masu yin wanga tada,
Halin fasiƙanci na ɓata gari
Nasihar da zan yi wa almajirai
Ku nisanci muggai fa ɓata gari
Da ka ga mutum bai da kunya guje shi
Ka sani yabo gun mutumin gari
Idan kai abota da yaro kamar ka
Ka lura da halinsa nan zahiri
Idan ka ga halin ɓata a gare shi
Guje shi ka nemi mutum na gari
Idan ka zai sa ka hanyar ɓata
Gare ka da zai zam shiga hatsari
Ka tanaji hanyar rabo da shiya
Kashedi da muggan ɗiya a gari"

Tirƙashi! lallai waƙa ba ta bar komi ba, dubi yadda waɗannan baitoci suke ta ƙoƙarin faɗakar da ɗalibai a kan su guje wa duk wani da ke da munanan halaye kamar rashin kunyya da fasiƙanci. Haka mawaƙin ya yi nasiha ga ɗalibai wurin yin abota da mutanen kirki tare da ƙaurace wa yin abota da mutanen banza. Dama babar matsalar da ɗalibai suke samu a makaranta ita ce, irin abokan da suke hulɗa da su. Wasu za su bar gidajen iyayensu lafiya lau, amma da zarar sun je makaranta sai rayuwarsu ta sauya saboda hulɗa da miyagun abokai.

Shi ya sa mawaƙin yake nasiha da cewa da zarar ya ga abokinsa na son ya sanya shi cikin miyagun ɗabi'u to wajibi ne ya ƙaurace masa. Haƙiƙa waɗannan baitotci za su taimaka wajen inganta kyawawan ɗabi'un ɗalibai kafin kammala karatunsu. Shi ma, Wazirin Gwandu Alhaji Umaru Nasarawa ya yi wata waƙa da yake cusa wa ɗalibai halin nagarta da nisanta su daga munanan halaye. Ga abin da yake cewa a wasu `yan baitoci:

"Wadda anka so almajiri
A isshe hali mai kyau garai.
Shi tsare mutumcin mallaminsa
Shi zan tsaron girma garai
A cikin aji a cikin gari
A ishe hali mai kyau garai
A cikin aji in an shiga
A ishe akwai himma garai".

Ka ga duk waɗannan baitoci suna bayyana yadda ya kamata ɗalibin ƙwarai ya kasance ne, kamar tsare mutuncin malaminsa ba

kamar yadda yake aukuwa a wasu makarantu ba., inda za ka ɗalibi yana aibanta malami wani lokaci har har da taɓa lafiyar malami. Hakazalika, ya zamo mai kyawawan ɗabi'u ya kuma zama mai himma a cikin aji duk mai irin waɗannan halaye da wuya a kama shi yana satar jarabawa ko wani abu makamancin haka. Har ila yau, ya bayyana wasu munanan halaye a wasu baitoci ga dai abin da yake cewa:

"Almajiri nan na daban
Shi kam hali mugu garai
Mugun hali ɓanan mutum
Ko da akwai ilimi garai
Balle daƙiƙi na shaƙiyyi
Babu amfani garai
Ashararu na shaiɗanu ne
An gane girman kai garai
Ga taƙala da yawan faɗa
Hakanan yawan ƙarya garai
Tsaransu bai da tagomashi
A cikinsu don fitina garai"

Waɗannan abubuwa da mawaƙin ya zano a cikin waɗannan baitoci abubuwa ne da ba su da amfani domin halaye ne na mutanen banza waɗanda suka iya kai mai aikata su ga mahalaka. Malam Sambo Wali Basakkwace a cikin wata waƙarsa da ya tsara, ya kawo illar shaye-shaye a wani baiti ga dai abin da yake cewa:

"Ga jin daɗin rayuwa samari ka ɓicewa,
Suna wasu `yan ƙwange-ƙwange don nuna ɓacewa.
Su sa takalma da ba wuya za a karewa
Su sha wata taba da hankali zai juyawa.
Su gigice don su sami damar ɓacinmu"
A nan mawaƙin ya kawo illar da shaye-shaye take jjawo wa kamar ɓacewar hankali da gigicewa da kuma la'antar magabata.

A wani baitin ya jawo hankalin shuwagabanni da malamai da hukumar makarantaa ya yi a kan su tsaya tsayin daka su kula da ɗalibansu a kan shhaye-shhayye ka da su bar su suna sha balle har su shuka wui-wui a makaranta. Ga dai abin da yake cewa:

"Zan College wajen yara, masu tattalin sura,
To Prinsipal gyara ka daina sa rashin lura
Har su kai ga shufka ta".

Haƙiƙa waɗannan baitoci da suka zo a cikin wannan aiki sun tabbatar mana da cewa rubutacciyar waƙa tana taka rawa wajen jawo hankali da wayar da kkann al'umma musamman dalibai, wajen gyara ɗabi'a da halaye a yayin da suke gudanar da karatunsu. Matuƙar aka yi amfani da darussan da suke a cikin waƙa.

**Kammalawa**

Wannan muƙala ta fito daa irin gudummuwar da rubutacciyar waƙa take bayarwa a fagen cusa kyawawan ɗabi'u da kuma nisantar da miyagun ɗabi'u ga ɗalibai. A cikin aikin an kawo baitoci da suka yi nuni da irin kyawawan halaye da ya kamata ɗalibi ya yi koyi da su a yayin da yake gudanar da karatunsa kamar biyayya ga malamai da natsuwa da ƙoƙari a cikin aji da tsafta da girmama sauran abokan karatunsa. Haka an kawo baitoci da suke ƙunshe da miyagun ɗabi'u waɗanda ya kamata duk ɗalibi na gari ya nisance su kamar shaye-shaye da rashin girmama na gaba da ta'addanci da zanga-zanga da sauaransu.

A ƙarshe, wannan muƙala an jawo hankalin ɗalibai da su kasance mutanen kirki abin koyi, saboda a kwana a tashi su ne

shugabannin gobe. Har-ila-yau, muƙalar tana kira ga gwamnatoci da hukumar makaranta da su sa tabaron kula wajen ɗaukar malami na gari. Domin Hausawa na cewa, "Inda sanuwar gaba ta sha ruwa, ta baya in ta zo ita ma nan za ta sha".

## Manazarta


Ado, A. (2019). *Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa*. Katsina: Government Printer

Bunza, A.M. (1994). *Yaƙi Da Rashin Tarbiyya, Lalaci, Cin Hanci Da Karɓar Rashawa. Cikin Waƙoƙin Alhaji Muhammadu Sambo Wali Basakkwace.* Lagos: Ibrash Islamic Publication Centre Limited.

Ɗangambo, A. (1984). *Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa*. Kano: Triumph.

Hamza, M.W. (1983). *Tauna Ka Hadiye Abokin Hira 2*. Zaria: Longman Nigeria Limited.

Inuwa, M.A. (2008). Gudummuwar Mawaƙan Hausa Wajen Cimma Burin Ƙudurin 2020. Mukalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani da Tsangayar Harsuna ta Kwalejin Ilmi ta Gwamnatin Tarayya da ke a Kwantagora.

Junaidu, I. (1981). *Ciza Ka Busa Abokin Hira 1*. Ibadan: Longman Nigeria Limited.

Kwantagora, S. (1986). *Yula Rubutattun Waƙoƙin Hausa Don Ƙananan Makarantun Firamare Na Jihohin Arewacin Nijeriya*. Ibadan: University Press Limited.

Muktar, I. (2005). *Bayanin Rubutattun Waƙoƙin Hausa*. Abuja: Country Side Publishers Limited.

Otitie, O. & Ogionwo, W. (1981). *An Introduction to Sociological Studies*. Ibadan: Heiman Educational Books Nigeria Limited.

Yahya, A.B. (2001). "Dangantakar Waƙa Da Tarbiyyar `Ya`yan Hausawa". Harsunan Nijeriya XIX Kano Center for the Study of Nigerian Languages Bayero University.

Yahaya, I.Y. (2002). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria: Kamfanin Buga Littatafai Na Nijeriya Ta Arewa.